Admin 004

Sardaunah Novel

GIDAN MATI
By Rufaydah Umar..
Young Writters Fanz
Page 1

Buguzum-buguzum ta sanyo kai cikin gidan tana wak'a.
"Ahayye iye nana..."
D'if ta dakata gami da sakin baki adalilin abinda ta hango a tsakar gidannasu.
Maigidansu Mati a k'ofar d'akin kishiyarta Abulle zaune su na hira da dariya. Ganinta ya sanya Mati yin tsuru da idanu yayin da ita kuwa Abulle ta washe baki, cike da dabara ta fiddo takardar naman da ta 6oye a bayanta ta warware ta d'auki tsoka d'ayan da ya rage ta jefa a baki ta na tauna gami da fad'in.
"Maigida kana burgeni, kana kawomin irin wanda na ke so."
Mati ya watsamata kallon muguwar mace, shaf a tunaninsa dagaske ta yarr da takardar tsiren, ashe makirar abinda ta shiryamasa kenan. Ya numfasa gami da share zufa ya na duban Nene batare da ya ce uffan ba.
Nene wacce zuciyarta ta gama kaiwa bango ta fisge mayafin kanta ta had'iye miyan da ya taru a bakinta tsabar na ranta ya biya ta ci d'amara ta hau tafa hannu.
"Allah na godemaKa da ka nunamin abinda ke faruwa a bayan idona! Ashe daman cuta ta ake yi ana dawowa idan bana nan? To yau dubunku ta cika Mati, yau sai an bambance tsakanin aya da tsak'uwa!"
Jin haka ya sanya Mati mik'ewa ya hau fad'an k'arfin hali da borin kunya.
"Ke ya isa! Yimin shiru dak'ik'iya kawai! Kin shigo gida ba sallama ba komai sai wak'en banza sannan ba ki tsaya kin ji dalilin dawowata ba yanzu kishi zai kaiki ya baro ki!"
Kafin Nene ta samu bakin magana, Abulle ta saki wata dariya irin ta wadanda duniya ta yiwa dadi.
"Kai namiji, namiji akace buhun k'aya. Sannunka munafuki, inace mun fi awanni biyu tare? Duk dai abinda za'ayi sai dai a yi don ba na tsoron kowace mai yanayin kul6a, miji ne mun yi aurenmu na soyayya muna zaune lafiya yana kawomin kayan mak'ulashe koda kuwa ba kwana na ba, sai a mutu!"
Da jin haka Nene ta zabura ta yi kanta ta na faman surfa ruwan ashariya.
"Yau sai na nakasa ki tsohuwar bazawara mai bin maza, saidai wannan tsohon gurgun ya k'ara haifar wata."
Ai sai su ka shiga kokawa, Nene ta daddage ta ba ta kyakkyawan cizo a mamanta wanda ya ke fata ce kawai. Wani ihu Abulle ta saki gami da fad'in.
"Kan uban can!" Ta cafki jan gashin kan Nene mai kama da gemun ɗan Bunsuru ta hau ja da k'arfi, ta kuwa shiga ihu har zaninta na fad'uwa sai ga ta zirr babu ko d'an bante. Mati ya tafi da gudu ya d'auki zanin ya na kokarin suturceta ganin magulmatan makwaftansu wato Gidan Delu da Gidan Shafa har sun soma lek'e ta Katanga.

"Menene haka? Ke Abulle don iyayenki sakarta!"
Wani turi da Abulle ta yiwa Nene sai kuwa ta jefata jikin Mati su ka yi kyakkyawan zubewa a k'asa abinka da siririn mutum. Da sauri Nene ta mik'e ta suturta jikinta ta na huci.
"Shegiya mai kalar mayu zan yi maganinki a gidannan, za ki san kin shigo gidan Nene."
Wani banzan harara Abulle ta watsamata sa'ilin da ta ke gyara zaman rigarta.
"Yanzu aka fara tashin hankula a gidannan muddin ba za ki fita a harkata ba. Mace ba ta ajiye komai ba sai ta ci ta yasar da k'aton kashi a masai! Gwara ni, tunda ko ba komai na yi 6ari an ga shaida!"
Nene ba ta jira komai ba ta nufi wajen girkinsu ta rarumo ta6arya ta taho a guje, ai Abulle na ganin haka ta fad'a d'akinta, ga shi ta kasa d'aga labulen kaban k'ofar d'akin hakanan kawai ta turo kyauren.
Nene ta tsaya ta na huci ganin Mati ya sha gabanta.
"Shegiya kai, ashe ke 'yar iskar k'arya ce, yo ki tsaya mana idan ban nakastaki ba anan."
"Haba Nene, ya isa hakanan, muje daga ciki ki ji."
Fad'in Mati hankali a tashe don shi har ya rasa ma yanda zaiyi ga makwafta 'yan gulma na kallo.
"Haba ke kuwa Nene, ki yi hakuri mana."
Fad'in Delu kenan cike sa tsegumi.
Wani banzan kallo Nene ta watsamata, sai lokacin ta lura da tarin magulmatan makwaftansu da ke lek'e.
"Kai! Allah Ya tsaremu da munafukai, mutane ba su ajiye komai ba banda munafunci da gulma, dadin abin dai mijina bai ta6a jibgata ba kuma bai ta6a haikewa wata ba."
Delu wacce tasan ita miji ke jibga ta ja tsaki ta ce.
"Oho dai! Duk acikin so ne." Daganan ta bar lek'en tare da yanmatan yaranta uku. Ita Shafa salin alin ta sauka ba ta ce uffan ba, to ina bakin magana tunda tasan da gaske mijinta kwarto ne na a kwantanta.
Dakyar dai Mati ya kashe rigimar tare da alk'awarin zai kawomata na ta k'unshin tsiren. Abinka da kwad'ayyiya kamar Asma'u a gari, ba musu ta hak'ura.
*** *** ***
Abulle ta ta6e baki.
Mati bai ko kula ba ya ci gaba da maganarsa.
"Sanin kanki ne dai Inna ba ta damu da zuwa k'auyen nan ba tunda Baban su Ladiyo ya d'and'ana mata zaman birni, yanzu kuma musamman don ni za ta zo ayi zumunci. Don Allah Abulle, ke ce k'arama, ke ce kuma ba ta sani ba, ki taimaka ku zauna lafiya har ta tafi. Sannan inda hali inason ayi wani abu."
"Menene shi?"
Ta fad'i da sauri.
Ya yi shiru sai kuma ya numfasa ya sassauta murya.
"K'aryar ciki."
Gaba daya ta zaro idanu ta na dubansa. Ta murza bajajjajen hancinta.
"Yi min gwari-gwari dai."
Ya hau bayani.
"Inna ta sanarmin cewa muddin ta tarar kema ba ki da ciki to lallai za'a samu matsala don kuwa

sai na sake ki na yi wani auren. Ni kuma kinsan dai ina sonki ina son zama da ke, don.."
"Tsaya tsaya Mati, shi ke nan wannan abu mai sauk'i ne zan yi, sai dai menene ribar? Wace kyautar bajintar za ka samu bayan hakan don nasan halinka, ba ka aikin banza."
Ya yi 'yar dariya ya shafi sumarsa.
"Kai kai Abu tawa ta kaina, kina da saurin fahimta kam. To bari ki ji, akwai wata tafkekiyar gona ta Inna da kuma gida da ta ke bayar da haya ana biyanta balas duk karshen wata, ba yanda ban yi ba akan ta bani gonar ta k'i, to ta tabbatarmin za ta bani har da k'arin gidan nan ya zama mallakin jikanta."
Abulle ai sai ta hau tsallen murna da sakin gud'a.
Mati ya hau rufemata baki a tsorace.
"Ke ki rufamin asiri kada waccan ta ji."
Tunanowa da Nene da ta yi ne yasa ta saurin sai ta kanta.

Page 2

Daga waje kuwa Nene na jin haka sai ta yi wuf ta fito daga maɓoyarta, can baya take zagayawa ta hau kan ɗan dutse tana kasa kunne a ƙaramar tagar ɗakin Abulle. ta na yi tana leƙa bayanta ko wani zai taho wucewa kasancewar daga nan ana hangen waje a dalilin gajartar katangar.
. Ɗakinta ta shige da saurinta, jiki na rawa ta hau sauke kwallayenta tana faɗin; "Idan sammako ku kayo, ni asubanci na yi."
Ta fiddo wani maganin gargajiya wanda tayi mugun tsanar warinsa, sannan ta mai da kayan ta afka garin kusan rabi a baki. Kan ka ce mene wannan cikinta ya murɗa ga yunƙurin amai da ta soma. Ai a guje ta fito ta isa gaban makwararar ruwa ta hau sheƙa aman iyakar ƙarfinta tana nishi yanda ta tabbatar za su tsinkaya...
"Ni fa kamar kakari nake ji." Cewar Mati yana kallon Abule.
"Kai fa daɗi na da kai har yanzu baka bambance kukan Jakinka dana Akuyar Delu."
"To idan ma itan ce kinyi zaune salon tamin ta'adin da ta saba?"
Ya faɗa yana mai mi'kewa tsaye, itama da sauri ta mi'ke tana mai rufa masa baya.
Ita ɗin ma ta wajen jin tahowarsu ya sata zubewa gefen kwatamin tana mai ri'ke cikinta da faɗin "Wayyo! Mati..."
Da gudansa ya 'kara so wajen yana mai janyeta gefe.
"Ikon Allah! Nene ashe ke ce. Sannu me kika ci ne haka?"
"Ba komai tun safe nake jin tashin zuciya da rashin jin daɗi."
Ta faɗa da ƙyar tana sauke numfashi.
"A'a irin wannan ciwon ai ba na shiru ba ne Nene, karki manta da haka Sahura ta mutu da irin shirun nan."
"To Mati ana ta kai wa yake ta larura? Taimaka min zakai Abule ta dubomin 'Yar Magaji, ji nake kamar ana daka yaji a kirjina."
"Huu'umm!" Abule ta faɗa tana tafa hannu.
"Ai wallahi da aiken kishiya gwamma na jibgi Uwar miji. Kai ni ban ma yarda da wannan ciwon ba. Saboda Allah Mati baka ji warin tazargaje ba?"
Ta faɗa tana mai ɗaɗɗaga hanci sama.
"Me kike nufi ne? Kinga Abule ban san fitina, ya mutum na halin ciwo kina kawo shashanci. Idan

na isa dake to maza ki je ki dubomin 'Yar Magaji."
.        Mintuna kaɗan Abule ta dawo da 'Yar Magaji biye da ita ta rataya wata tutturna jaka me kama da ta wazirin Sarkin kutare.
Kallo ɗaya tama Nene maƙaryaciyar zuciyarta ta kisa mata menene,
dan haka ta kalli Mati da murmushi.
"Malam ai ba wata larura ba ce mai girma, ƙaruwa ce zaku samu, a taƙaice dai Nene ciki gare ta har na tsawon wata biyu."
"Kan babban bala'in can! Alkur'an wannan ƙarya ce."
Abule ta faɗi tana mai buga tsalle gefe, kafin kuma ta yi ɓarin da Nene ke kwance.
"Ke Nene ki ji tsoron Allah, ina ce ba shekaranjiyar nan muka gama rikici kan tsumma na da kika yaga kikai kunzugu da shi ba?"
"Wayyo Ni Abule! Yau na ga abinda yafi 'karfina, wai cikin ma har kinsan ya yi wata biyu sai ka ce wacce kika haɗa iri da Mayu. ke kam 'Yar Magaji anyi tantiriyar ma'karyaci wallahi. Matar da ake raɗe-raɗen Aljanu sun sace mata mahaifar ne ke da ciki?"
"Ke! Ke! Abu kin cika mana kunne da shegen karaɗi. Ki tsayamana abu abin a sannu idan ma ƙaryar ce ai 'Yar Magaji za ta faɗi.
"Wane irin bi-sannu Mati? Ai fa magana ta riga ta ƙare, Nene dai ciki gare ta, maganar ganin jini kuma wanann a bayyane yake, ko Magaji ka tambaya zai idar maka wannan zance. Lalle ne akwai Matan dake jini da ciki. "
"Ke kuma Abule da kika haɗa Ni da Maita ina jin dai tsohonki shi ne Bazawari na? Dan haka bushiya dai ba zata wa Kunkuru gorin ƙafa ba , ko zaki mutu dai Nene ciki gare ta na wata biyu."
"Kai kuma yanzu ya rage naka sai ka dinga mata abinda take so. Ni kaga tafiya ta."


"To ai sai ki kauce daga samanmu tunda dai shegen baƙin cikinki ya jawo kinji abinda Tsohonki ke aikatawa a waje."
Mati ya faɗi yana hararar Abule da tayi tsaye hannu bisa ƙugu tana jinjina maganar 'Yar Magaji.
"Oho dai, daɗin ta Bazawari aka ce ba Ɓarawon Jakai ba."
Ta faɗa tana hararar Nene dake yatsine-yatsine.
.
"Kyale ta kinji Nene uwargidan Mati, muje na raka ki ɗakI ki kwanta, daga yau ko tsinke ban yarda kin ɗage a gidan nan ba, wanda ba zai iya gani ba yayi zuciya mu gani a ƙasa." Ya faɗa cike da lallami.
Ita ɗinma miƙewa tayi cike da kwarkwasa har da riƙe rigar Mati. Gab da zata ɗaga labulen kabar ta ne ta waigo ta kalli Abule fuskarta ɗauke da murmushin kaɗan kika gani.
Dogon tsaki itama taja tana hararar ɗakin bayan shigewarsu. "Wai Kura ce ta samu damar miƙe ƙafa, ayi dai mu gani, muna nan za ka zo kana min 'yar murya. Har yaushe ma akai daren?" Jin shiru ba su amsata ba sai tashin dariyarsu da take ji ne ya sata juyawa a fusace zuwa na ta ɗakin.
Kwana biyu gidan shiru daga uhumm sai hu'umm wai uwargulma tayi cikin shege. Duk san Abule na ta gane gaskiyar cikin Nene abun yaƙi yiwuwa. Sai ma barinta da takaicin arba da ledar Burodi da Tsire da take yi kullum safiya. Idan ma ta yi dakon hana ido barci dan a kasa da

ita Mati baya shigowa gidan sai dare ya raba, kafin ta gama barcinta ya kaɗa na sa Jakan yayi gaba tsabar rashin gaskiya.
Sauri take ta isa gida, dan ta fara gwada maganin saka laulayin da Gwaggonta ta bata ta dinga shansa duk dare, bayan ta sanar mata da abinda ke faruwa a gidansu. Ta tsinkayi muryar Delu na kwaɗa mata kira.
Kamar ba za ta tsaya ba, sai dai taja tunga ganin Delun harda ɗan gudunta.
"Uhm! Tunda na taho nake Addu'ar Allah ya sa na ganki, dan kuwa ba za ai wannnn cin Amanar a gaba na ba."
Gabaɗaya ta mai da hankalinta kanta
"Me ya faru Delu? Na sanki baki maganar banza."
"Ke dai Allah ya raba mu da Miji mai ɗabi'ar hankaka. Mati na gani yanzun nan gun 'Yarbaiwa mai Fara ya sai har ta Naira Hansin wai Uwargida ke kwaɗayinta, baki ganta ba fal ledar..."
"Fara fa kika ce? Farar da tunkan muyi aure yake min alƙawarin cinta?" Ta tari numfashinta.
"Idan ƙarya nake miki wannan zance tsawar bana ta sauka gonar Malam Alkur'an."
"A'a me na jan masifa? Zai yi fin haka ko dan ya nunan shi Namiji ne kwandon zawo, barni da shi, yau ko zai mutu ba za ta ci Farar nan ita kaɗai ba. Ke har ke sai kin ɗanɗana, na gode miki Delu, bari na ƙarasa gidan.
Da sallamarta gidan ta yi jifa da kallabin kanta gefe, luma yatsunta ta yi cikin gashinta ta fara wargaza shi, kan kace mene wannan ta tada hankalin gashinta ya yi tsaitsaye tamkar gemun Mahaukaci da ya shekara ana jifansa. Nene dake gefe ana ƙoƙarin sai ta kai, sai gani tayi Abule ta zube tana wani nannaɗewa, doka ihun da zata yi sai ga shigowar Mati yana mai da aljihunsa baya. Ganin Nene jiki na ƙyama ya sashi yin wurin Abule yana salallami.
"Karka ƙaraso! Kana ƙarasowa idan muka fyauɗe ka sai ka dangana da Gyatumarka" Yaji murya na gargaɗinsa kamar ta Kuyangar Kutare.
Turus! Yayi ƙafafuwansa na rawa kafin kuma ya zube ƙasa yana kallon yarda Abule ke naɗewa bakinta na dilalar yawu.
"Kiyi haƙuri Abule wallahi bansan kina da larura ba."
Ya faɗa kamar zai fashe da kuka.
Taja majina.
"Kai! Ka iya bakinka, wanann ba lalura ba ce, kai ne ka kira mu da kanka da kake taɓa mana Goɗiya kana sa ta kuka."
Ta faɗa tana zare manyan jajayen idanuwanta.
"Ƙarya take min bantaɓa sa ta kuka ba, Nene shaida."
"Munafuki menene wannan a aljihunka na hagu?"
"Fa..fa ...fara ce."
"To wa ka siyo wa?"
"Abule mana, ita ce Amarya ta da bana iya motsi sai da ita."
"To bawa waccar ta kawo farar nan gabanmu, gargaɗin ƙarshe kuma ka kuskura ka ƙara kawo ko Dusa ce ba ka haɗa da Goɗiyarmu ba sai mun musanya mata yaron cikin da take ɗauke dashi da Kadangare."
"Ban..ban..gane ba..."
"Au! Dan fitsara ma baka San Goɗiyarmu na da cikin ka ba?"
"Na sani, ku yi hakuri. Ke Nene miƙa musu Farar mana."

Ya faɗa yana jefa mata kullin ledar dake ta kyallin mai .
Abule ta kalla idonta kamar zai faɗo dan tsoro, gani take kamar bakinta ma ya koma gefe, dan haka ta Yi baya cikin hawaye.
"Ba zan iya ba Mati."
"To kuwa zan fita na barki da su, ki miƙa musu ko za su tafi."
Ya faɗa da tsawa.
A ɗarare ta miƙa ledar gaban Abule dake naɗe, a guje ta juya zuwa ɗakin ta ta lafe bayan kaba tana hangen su.
Ƙatuwar Hamma Abule ta saki, kafin kuma ta ɓingere gefe maƙale da ledar farar ta. Akwai alamun Borin ya sauka.
*** **** ***

Page 4

Assalamu Alaikum mutan gidan." Fad'in 'yar doguwar dattijuwar kuma tsamurmura mai sharɓa-sharɓan tsagu a gefen bakinta, bak'a ce wuluk kamar d'anta Mati. Mati ne a gaba d'auke da k'aramar akwatin kayanta, ita kuwa tana biye da shi a baya.
Abule ta soma fitowa daga d'aki sai Nene daga band'aki suka saki baki suna kallonta.
'Ikon Allah, wai na kwance ya fad'i.' Cewar Abule kenan a k'asan ranta ganin shigar da surukar ta su ta yi, wata k'aramar Atamfa Super ce ajikinta an mata dinkin riga da siket sai wani babban mayafi da ta yafa a kafad'a ba rufin kai ba. Fuskarnan ta sha farar hoda, ba'a gane wa sakamakon bakin fatarta da ya ciza saidai kuma kana gani ka rantse yanayin hunturu ne wanda ya yi sanadin da fatar fuskar nata ya bushe ya yi furu-furu, ga uban jan janbaki da ta lafta a le66anta masu tudu.
A hankali Nene ta maida dubanta ga Abule, akayi sa'a itama ta kalleta sai kuma suka sauke ajiyar zuciya kafin kowaccensu ta shiga rububin tarbarta da amsa sallamarta.
"Waalaikumussalam, lale maraba." Fad'in Nene kenan ta karasa bakinta a washe ta kar6i akwatin Inna, caraf itama Abule ta sanya hannu da zummar kwacewa ta kai nata d'akin.
"A'a menene haka? Yaushe akayi daren kuma da har ace gari ya waye? Malama sakarmin." Cewar Nene ta na k'ara jogana akwatin a jikinta.
Dole Abule ta saki tana harararta ta karasa wajen Inna cike da kissa ta ce.
"Maraba Inna."
Inna ta hau k'arewa Abule kallo, eh kam ta yarda da rahoton da Aminiyarta Ladidi ta kai mata game da Amarya d'an nata. Ta tabbatar mata tafi Nene tsafta kuma ta ga alama. Sai dai kuma ta kasa fahimtar me ya ja Mati ga aurenta? Wannan abu a dunk'ule haka?
"Yauwa sannunki kema."
Ta fad'i tana mai k'arasawa ta zauna a saman tabarmar da aka shimfid'a. Nene za ta yi ciki da kayanta ta yi saurin dakatar da ita.
"A'a 'yarnan dakata."
Zani na kuncewa tana sake d'aurawa ta karkata k'ugu ta tsaya gami da dire akwatin tana jan majina.
"Na'am, to."
Inna ta yamutse fuska.

"Ai kuma sai dai wannan karon ki hak'ura don a d'akin ita 'yar uwarta ki zan sauka. Na gayamaki bana son kwana kan wannan gadon naki mai warin hammatan wanzamai, da kyar idan kin chanja wannan tsohon zanin gadon wanda na gama yayinsa tun jegon mijinki. Ba wa abokiyar zamanki akwatin na ga na ta kamun ludayinta."
Ai sai Abule ta kece da dariya, kallon banzan da Inna ta watsamata ne ya sanya ta nutsuwa. Nene ta cika ta yi tam! Yau ita Inna za ta ci wa fuska akan Abule? Lallai ya dace ta zage damtse.
Tana numfarfashi ta zauna, Inna ta dubeta sannan ta k'ara duban Mati.
"Wai ni Mati wacece me juna biyun a matanka?"
Mati ya hau washe baki.
"Ai duka biyun ne."
Inna ta kwalalo idanu cike da mamaki tana duban Nene, karshe ta sauke idanunta akan Abule da ta zauna tana wani sussunne kai ita a dole kunya. Sai kuma ta hau tafa hannuwa da shewa. Farin ciki ya cika su don a zatonsu ta yarda suna da cikin. Sai dai ga Inna kuwa sam zuciyarta ba ta amince Nene na da ciki ba, shekaru nawa da aka yi ta rad'e-rad'in ba ta da mahaifa, ai kuma ta saka ayar tambaya. Dabara ta zo wa Inna.
"Yau na ga abin al'ajabi, to ai shikenan, zama ya kamani a k'auyen nan duk da ba na so, amma zan zauna har na ga 'ya'yanka Mati."
Hanjin cikin Nene da Abule ya kad'a sai dai kowaccensu ta yi fuska. Mati kuwa wani dad'i ne ya mamaye zuciyarsa ganin burinsa ya kusa cika.
Abule ke da girki ita ta shiga hidima da Inna, Nene kuwa d'akinta ta fad'a tana tunanin mafita nan gaba.
*** *** ***
Bayan kwanaki hud'u da zuwan Inna ana zaman lafiya kowacce ta ciki na ciki. Karshe kuma sai Mati ya tsuro da wuni a d'akin Abule wai hira da Inna, haka za ta yi ta tsinkayo dariyarsu.
Da abin ya isheta ta shirya ta nufi gidan 'Yar Magaji don neman mafita. Tana isa ta zayyanemata komai, 'Yar Magaji ta buga uban tsaki.
"Ke ce ai ki ka yi sake da ba ki mallake Mati tun fari ba, yanzu da komai zai zo ma ki da sauk'i."
Jin haka Nene ta gyara zama.
"To yanzu ya za'ayi."
'Yar Magaji ta d'an yi jim, sai kuma ta saki dariya ta mik'e ta fad'a d'aka. Can sai ta dawo d'auke da k'ulli ta mik'amata. Nene ta hau jujjuyawa.
"Na menene?"
'Yar Magaji ta d'an murza hanci tsabar warin da bakin Nene yake yi kamar na 'yan ga ruwa.
"Kinga wannan, k'asar k'ark'ashin gadon ma'auratan da suka tsufa tare ne suna soyayya, matuk'ar kin yi turare da shi na kwanaki uku Mati ya kusanceki to an gama."
Nene ta girgiza kai.
"Matsalar mun fi wata biyar bai nemeni ba, ni kinsan na tsani a maisheni jaka."
Wani kallo 'Yar Magaji ta yi mata sai kuma suka kwashe da dariya 'Yar Magaji na kauda kai.
"Dad'ina da ke ba dai warin baki ba."
Nene ta muskuta tana shafa bakin.
"Um to ya na iya da abinda ya fi k'arfin wuta?"
Ta6e baki 'Yar Magaji ta yi.

"Ke ki ka so, ni yanzu dai kinsan ina jiran kaso na, makira ai ina shigowa daman na ga yanayinki na gane makircinne ya motsa."
Nene ta dara.
Suka gama k'ulle-k'ullensu dai Nene ta koma gida da zummar soma gabatar da aiki.

Page 5

©BINGYEL FULANI & RUFAIDA OMAR
Inna ta d'aga hanci sama taja iska, sai kuma ta furzar ta baki tana hararar kwanukan da Nene ta aje gabanta.
"Uhm ni wai da mushe kikai miyar ne Nene?"
"Me kika gani Inna?" Nene ta fad'a tana so sa kai.
"A'a gani nayi tunda kika doso gurinnan ya cika da tsami da k'arni tamkar wacce ke aiki a kwata ko mutuware."
'Ai fa, komai na yi ban burge ba, to ai sai dai ki mutu, aikin na Mati ne, mallaka kuma tawa ce, sai shegen kinibibi da wani bakinta kamar na ba'kar Akuya...' Ta faɗa da gunguni
"Me kike cewa ne?"
"A'a cewa na yi Binta Sudan ne na balbala a jikina saboda kiji ƙamshin."
"Ko kuma Binta Maliya ba? To wanann dai ƙarni yake sai a sake lale, ki kwashe kwanukan nan daga gabana, anjima zansa Mati ya karbomin Abincin daga gidan Larai."
"Uhm gaba ta kaini, dama ke na tsamewa kai da ƙafar kazar." Ta faɗa da 'kun'kuni tana tattara kwanukan.
"Baki ji ba" Inna ta fad'a
"Ina ji Inna" Ta fad'a tana gabda barin d'akin.
"Idan gyaran zaki yi ki fara gyara can cikin, shi ne ko da kinsa turaren zamu ji dadinsa, amman wanann in gayamiki gaskiya yau sai an turaramin dakin nan da miski zan iya zamansa. Yanzu haka sai na sha kanwa sabida kumburin ciki."
"To masharranciya." Nene ta fadi a hankali tana barin d'akin a fusace.
Abule dake maƙe a gefe tana sauraro ta k'yak'yace da dariya tana juyawa Nene mazaunai.
Nene ta yi kwafa tana gyaɗa kai, kafin kuma ta yi dakinta tana mai sauke kaba.
Gab da Maghriba Abule na tsakar gida tayi ɗaurin kirji, da zabira a hannunta tana tsifar kai. Can daga k'ofa kuma Nene ce zaune tana gyaran Tafasa tana yi tana sakin habaici a waƙe.
"Munafuncin dodo dai mai shi yakan ci, yau ba jumma'a ba idi ba, ba kuma kwanan mutum ba ya d'au niyyar wanka harda tazar kai na asara." Nene ta faɗi da karfi tana hararar Abule."
"Oh ni Abu? Lalle idan ta karewa kare barin haushi yake ya koma tunkuyi, na ga dai abin rabo ne auran Mace da ciki. Ki gwada naki salon mana mu gani, ai wani asirin baya ci da turaren hayaki sai an had'a da yan dabaru."
"Uban wa ke asiri da turare?" Nene ta faɗi a fusace tana ture fai-fain tafasa gefe."
"A'a ai kinji matsalarki baki cin ribar magana, yanzu mene na sakin na maguzawa a wannan hirar? Ni kinga wucewata yin abinda zai fisshe Ni. Ta faɗa tana mai sunkutar bokitinta ta fada Makewayi.
Nene ta ciji yatsa tana mai tura baki gaba, sai kuma idanuwanta suka sauka kan kayan da Abule ke d'orawa saman yar katangar bandakin ta langa-langa. Abin mamaki harda wani tsohon

dankwalin wata atamfarta me fanteka da mati ya sa mata tun a toshi. Har dai ta juya zata wuce, sai kuma dai ta sake juyowa tana  kallon katangar zuciyarta na kiyastamata abinda Abule ke yi da kaya haka. Nan fa idanuwanta suka sake sauka kan wata tsummar rigar Mati da tun yana Saurayi ta sanshi da ita. Wani makirin murmushi ta saki da ta gama hasaso abinda take zato. Ai sai tayi gun 'yar katangar a hankali ta janye kayan bata bar mata komai ba sai zanin da zata yane jikinta.
Da sauri tayi ɗaki gurin Inna dake gyangyadin shaiɗan na gabda Maghriba. Itama Innan sai da ta firgita na ganin yarda Nene ta fad'o Mata ba ko gafara dai.
"Lafiya Nene kika katsemin barci haka dan rashin mutunta Uwar Miji?"
"Bari dai Inna, ai abinda na gani yau idan ban sanar miki ba na cika ma-ci Amana, na rantse miki da izifi sittin Abule cikin zani gare ta. Idan baki yarda da batunnan ba biyoni kofar Makewayin ki gani."
Inna ta watsa mata wani kallo she'ke'ke, sai kuma ta mi'ke tana tura d'aurin kallabinta gaba."
"Muje na gani." Ta fad'a tana yin gaba.
Abule da ta gama jika-jikan ta mi'ke za ta mai da zannuwanta ta d'aure yanda ta saba, ai sai ta tarar babu, ta d'auka ko baya suka faɗa dan haka ta fito a sad'ad'e tana Addu'ar Allah ya kau da idon Nene har ta kwashe. Sai dai fa turus! Ta yi ganin Inna da Nene tsaye tana sakar mata dariyar Mugunta. Jiki na tsuma ta sunkuyar da kanta 'kasa.
"Shegiya guntuwa me bakin hali, abinda ban zaci gare ki ba sai gashi ya tabbata gunki. Uwar wa ta koyamiki wanann kinibibin ko dan ganin yar uwarki na da cikin? Inna ta fadi tana mai kai mata rankwashi a jikakken kanta.
"A'a Inna lafiya kike bugurmin Abule" Mati ya faɗa da shigowarsa kenan.
"Zaka rama mata ne? Sha-sha-sha kawai, Matarka na cikin Zani dan sakarci ka kasa gane wa."
Ya kwalalo ido yana dubanta, sai kuma ya hau sosa kai yana noƙewa.
"A'a Inna ya za ai na sani, abinda rabon da ayi abu tun watan shekaran jiya.
Ai sai Inna ta hau tafa hannu da Sallallami.
"Haka Auren ya mayarmin kai Mati sai abinda Mace take so?Mene amfanin auren idan ba za ka taki mace tamkar gona ba? Ya kinan baƙar Munafuka sai kin faɗimin abinda kike bawa dana da har kike juyashi haka ko kuma ki tafi gidan Ubanki wallahi."
Ta faɗa tana jawo gashin Abule. Da sauri Mati ya shiga tsakani yana faɗin "Sakarta Inna."
Da dai Abule ta fito daga hannun Inna ai sai tayi kan Nene dake ta sheka dariya a fusace tana faɗin " Bazan fita Ni kaɗai ba sai da ke bakar mujiya muga naki cikin mana in gaske ne." Ta kai mata wawura.
Nene ta kankame jikinta tana ture Abule, ta ɗaga hannu zatai naushi, Abule tayi nasarar bankare hannun ta kuwa gatsa mata cizo a hammata da dazunnan ta barbadawa hammatar toka dan ta rage tsami, ai kuwa bata ɗaga bakinta gurin nan ba sai da ta cisge gashin hammatar Nene har jini yayi tsartuwa.
Nene ta saki ihu tana dafe hammatarta. Abule kuwa ta yi wuf! Ta fisgo zanin Nene sai ga tullin tsummokara ɗaure a ciki. Wani abin mamakin har da wani koren Gajeran Wandon Mati da ya gaje shi tun gurin ƙaninsa yasha doyin jakai da warin fitsari, da Mati ya shafe shekara yana nemansa, yau sai gashi a cikin Nene ɗaure...

Inna ta hau tafa hannuwa tana salati iyakar k'arfinta, kan ka ce me magulmatan makwaftansu sun hau lek'e cike da al'ajabi.
"Yau na ga abinda ya fi karfina ni Uwar biyu! Kai! Kai! Wallahi ba za ta sa6u ba, Mati!"
Ta juya ga Mati wanda zufa ke ta karyomasa, gabadaya ya susuce, daman ita Abule ya san k'arya ce ta shukamasa musamman da ya ji tana maidawa Delu irin tuggun da ta shirya na iska, ita kuwa Nene bai ta6a kawowa k'arya ta ke ba, a zatonsa idan Abule ta ɓata rawarta da tsalle to yana da mafaka a wajen Nene. Sai dai ashe dukkansu taron na ayya ne.
"Eh dole ka rasa bakin magana mana! To wallahi ba za ta sa6u ba! Ko ka k'ara aure ko kuma ka saki kowace shegiya ta koma akurkin ubanta. Za6i ya rage naka, yanzu na ke son amsata."
Inna ta k'arashe tana gyara zaman siket dinta na buje. Nene da Abule suka shiga tashin hankali, kada fa su yi biyu babu.
"Kai nake sauraro ka tsayamin k'erere kamar liman ya manta Fatiha."
Mati ya saci kallon Matansa, to da ya rasa tafkekiyar gonar Inna da kuma gida ai ya gwammace ya k'ara auren ya samu haihuwa.
Ya mai da idanunsa kan Innarsa.
"Shikenan, ki nemo min mata."
Ai sai Inna ta rangad'a gud'a.
"Ayyiririririii! Haba ko kaifa, yanzu na tabbatar da cewa kai jini na ne. Sai ka shirya don kuwa yanzu za ka yi aure."
"To amma..."
"Amma me? Inna ta katseshi tana harararsa.
"A'a wai dama gani na yi su biyun ma mangalar jakai na biyu bata iya rikesu da ita, shi ne nake tunanin kar ta ukun ta shigo kuma idan ina cin abinci sau biyar a rana na dawo sau uku."
"To batunu ƙiyama sarkin ci, in ce dai gidan nan nawa ne?"
"Naki ne har ni d'inma." Ya faɗa yana dukar da kai.
"To tunda ni zan ma auren mene na tunani? Idan ta ciyarwa kake zan ƙarama akuya da rago ka kiwa ta. Ina ce dai shi ke nan?" Ta waigo ɓarin da su Abule ke tsaye.
"Ku kuma sai ku shirya don kuwa falleliyar budurwa zan samar masa, ba irinku zawarcin titi ba."
Bak'in ciki ya turnuk'e Nene da Abule. Musamman Nene da ta tabbatar bata kai na ta matancin ba, amman dai ai ita ce ta fari, kuma ma ta toshe yanda ba za a gane ba, don haka ta karkata baki.
"Allah na tuba ko dubu zai auro ba kamar ni a zuciyarsa, ni ce dai Nenen Mati, kaf k'auyennan an shai da soyayyarmu."
Inna ta bankamata harara kawai ta wuce d'aki. Shi ma Mati da saurinsa ya fita ya hau jakinsa ya fice. Abule ce ta saki shewa.
"Aikin banza wai bille a d'uwawu, duk dai abinki bai sanya an fasa auroni ba, dad'in abin ma ba abinda bansani ba. Ina ce da sa hannun aljanu da 'yan bori a aurenki da shi ko?"
Nene ta fusata, za ta kai mata bugu tuni Abule ta nufi d'aki, ta mai da dubanta ga masu lek'e.
"An yi asara munafukai da tsakar rana babu ko kunya!"
Babu wacce ta tankamata acikinsu, ta gama haukanta ta fad'a d'akinta.
BAYAN WATA BIYU
Ta faru ta k'are, duk wani shiri da gyare-gyaren da ya dace a yi na zuwan Amaryar Mati an

kammala, amaryar ba wata bace illah Faɗime d'iya ga aminiyar Inna, Ladidi. Daidai da lefe Inna ce ta koma birni tare da Ladidi suka haɗo. Abu kamar wasa dai aka sanya biki sati biyu, duk irin borin Nene da Abule bai sa an fasa ba, ganin babu Sarki sai Allah ya sanya suka hak'ura.
An kawo Amarya lafiya lau da gud'a da komai, cikin 'yan rakiyarta har da Shafa da Delu.
Kwanan Amarya d'aya a gidan Inna ta tattara ta koma birni da zummar sai nan da sati biyu za ta k'ara lek'owa.
Nene na zaune ta tsefe kitsonta wanda ya kusa shekara yayin da Abule ke kwance saman tabarmar kaba tana jifanta da wak'e-wak'en habaici tana ramawa suka tsinci muryar Mati da Amaryarsa suna shek'a uwar dariya, suka dubi juna da sauri kamar wadanda aka mintsila suka nufi k'ofar d'akin nata har suna bangaje juna, ƙarshe dai suka nutsu suna lek'esu.
Amarya Faɗi ke kwance saman cinyar Mati, shi kuma yana yagar tsire yana sa mata a baki suna hirarsu cike da nishad'i. Nene ta dafe kirjinta gami da had'iyar yawu. Ba ta jira komai ba ta yi wuf ta shige ganin haka Abule ta ja baya tana mai rike ƙugu.
"Kan uban can! Wato Mati dama amanarmu ku ke ci? To wallahi ba za ta sa6u ba! Sai dai ayi raba daidai!"
Za ta d'auke ledar naman Faɗime ta cafke hannunta ta mik'e tsaye.
Baki Nene ta saki ganin shigarta.
"Riga da wando a gidan nan? Jakar Uba! Mati karuwar birni Innar ta auromaka ashe banda labari?"
Harara Mati ya sakarmata bai ce komai ba don wani sa'in yana shakkarta. Faɗi ta kauda fuska gami da murgud'a bakinta da ya sha jan baki.
"Ke Malama don Allah ki bar nan wallahi warinki na tayarmin da zuciya. Ga dukkan alamu dai ko wankan tsarki ba kya yi."
Ta saki hannunta.
"Kuma wallahi ki ka k'ara ta6a ledar nan sai na miki ihun mahaukaciya. Ce miki akai Ni haɗamammiya ce irinki? Ga naku kason can a gefe dan bazan yarda Miji na ya tashi da shanyayyen ɓarin jiki ba ranar gobe ƙiyama."
Nene ta hau tafa hannu da shewa.
"Hehehe!  Yau nake ganin bariki a gidan nan, ashe kuwa yau wata za ta bi tsohon najadu barzahu. Idan kin fasa kirana mahaukaciya ba ki cika d'iyar Ladidi mai siyar da kayan maye ba!"
Fad'in haka keda wuya, ta kai hannu za ta d'auki ledar, Faɗime ta damk'i gashinta ta mai da ta baya, tayi taga-taga za ta fadi k'afar Mati dake ƙasa ya miƙe ta kwashe ta sai gata Tim! A ƙasa tayi zaman 'yan bori.
Faɗi ta juya da Mini-minin idanuwanta ta dubi Mati "Sannu Maigida bata dai jima ciwo ba ko?"
Mati ya washe baki ya ce "Faɗi Amarya ina gabanki ai bana jin ciwo."
Ta yi masa far! Da ido ta ce, "Mai gidana na sha ce maka Timah zaka dinga kirana yarda kawuna na birni ke faɗi.
Taɓɗijam! "Yau na ga sabon salo wai tafiya bariki da Uwa" Cewar Abule daga bakin ƙofa.
Amarya ta waigo ga Nene dake baje ƙasa tana cije baki, "Ke kuma ki ci gaba da shiga shirgi na, wallahi da ruwan sanyi zan dafaki dan ban iya dambe tsakar gida ba, balle na haifawar maigidana talauci, ku da kuka saba kuje can ku ƙarata, ga tsiyarku nan." Ta faɗa tana tura musu kasonsu na tsire.

"Maigidana Randar Zuciyata, Idan ka fita kaje shagon Bakari Mai Ashana ka ce a baka Makilin da Burushi." Mati ya washe baki yana kallon kwalelen kanta da yasha zanen shuku yana ta ƙamshin Karkar.
"Wani sabon Abinci ne muka samu Amarya Timah?"
Ta yi far! Da ido "a'a kai dai jeka kawo za ka ga abinda zan maka da shi."
"To shi ke nan, bari na yi wanka sai na fita na siyomiki, kinsan tunda na sameki bana iya fita banyi wanka ba.
Ta yi murmushi "Yauwa kama tunamin abinda na ce zan nuna maka rannan, muje Makewayin na maka kaga sai na cuɗamaka baya ma."
Ta faɗa tana jawo hannunsa su fita. Fisgewa ya yi yana nuna mata waje da baki, sai kuma a hankali ya ce "Ki rufan asiri safiya ce fa? Kinsan su Nene sun tashi kar ya zama abinda zan kasa cin abinci yau."
"Haba Maigida Ni wallahi kanamin irin wannan sai in dinga ganinka ragon maza, ranar kwana nane fa, kuma baka shiga haƙƙin kowa ba dan ka shiga Makewayi da ni, Matarka ce ni, ba ta aro ba, ko ta titi, kuma ko su ka shiga Makewayi da su ba abinda zai dameni tunda na san aikin lada ne.
Ya zare ido yana dubanta "Da gaske aikin lada ne?"
"Kwarai kuwa, ai zaman Aure indai ba cuta lada gare shi."
"Au to muje, amman dan Allah saɗaf-saɗaf bana so Nene ko Abule su tsinkayi motsi na.
"To shi ke nan muje" Ta faɗa tana me yin gaba. Ruwa ta tuttula daga tulu a ɗan kwatashin wankan na su, ta sunkutu ta yi Banɗakin da shi, shi kuma Mati ya hau kewaye tsakar gidan, da dai yaji kamar babu motsi ko daga ɗakunansu, ai sai ya yi wuf! Ya faɗa Makewayin.
Abule ta yi miƙa ba salati ba rufe baki, ta miƙe tana mai riƙe mararta sakamakon fitsarin da ya riƙe mata ita. A hankali ta fito waje, ganin ba kowa ya sa ta tsugunna nan gefen kwatamin tsakar gidan ta tsiyaya abinta, ta wawwatsa ruwa ba ko cuɗawa ta miƙe, za ta koma ɗaki ta jiyo kamar kacaniya a Banɗaki, a zatonta Kajin maƙotane ke kacaniya, sanin da ta yi sunsha faɗawa wawakeken masansu azo a yi ta hayaniya ya sa ta zari sanda da sauri ta yi makewayin. Sai dai fa turus! Ta yi tana sakin wani razanannen Ihu ganin Mati zaune a dutse daga shi sai gajeran wando, Amarya Timah kuma duƙe saitin hammatar Mati da wani ɗan ƙarfe a hannunta tana ta kwasar gashin hammatar tana hura masa iska, shi kuma yana dariya gami da fadin "Wai, ci gaba, dadi wallah."
A firgice Fadi ta yada ɗan ƙarfen saboda yadda ihun Abule ya kiɗimata, Abule kuwa da ƙyar ta jawo sauran numfashinta tana son daidai ta kanta, sai kuma ta ɗaga sanda ba tai wata-wata ba ta saukewa Fadi ita a kafaɗarta.
"Sai na nakasaki baƙar mujiya me salon karuwai kawai, dan Ubanki ce miki akai nan bariki ne da zaki shiga wanka da Mijina, ko kuwa ce miki akai ni ɗin zan yarda."
Ta sake ɗagawa za ta rafka mata Mati ya riƙe sandan jiki na ɓari, "Karki kuma dukanta, zan fa rama mata, ke Abule ki fa fita idona da wanann jahilcin na ki, baki san aikin lada ba ne take yi? Ba na son sakarci fa." Ai sai ta yi baya tana kallon Mati sama da ƙasa, kafin kuma ta rangwaɗa guɗa.
"Ahl lalle Mati yanzu na san ka ɗauru tamau! a Minjaye, yanzu saboda wannan me zubin

botoramin kake cewa zaka dake ni, Ni Abu? Da ka ce aikin Lada na ga dai kwanana ya shiga daga sanda aka kira assalatu."
"To na ji, yanzu dai wuce ki tafi haka ba zai ƙarawa faruwa ba."
"Bazan tafi ba, Ni fa idan ba jini na fidda mata ba bazan ji daidai ba."
"Haba Abu tawa, na ce kije dai, da daddare zaki ji saƙo."
Ta ɓallawa Faɗime harara dake dafe da kafaɗarta, ki sake gwadamana karuwanci gidan nan ki gani, wallahi na lahira sai ya fiki jin daɗi, shegiya da wani idonki kamar tsaka ta saka kwai."
Af! Abu mai sauki, wai kura ta zo gidan Maharbi, idan karuwancin ne ki gwada naki mana mu gani, ai wallahi babu wata me siffar Fanteka da ta isa ta hanani kula da Mijina. Aikin lada ne yanzu na fara, wanann sandar kuma bashi kika ci." Faɗi ta faɗa tana murguda baki.
Sanin Mati ba zai barta ta sake taɓa Faɗi ba, ya sa ta juya ɗakinta takaici fal ranta.
** ** **
Tun bayan da akayi cacar baki tsakanin Abule da Fad'ime gidan ya k'ara kacamewa. Tsakanin Abule da Nene sai ka rantse tun da can kansu a had'e yake tsabar amincin da suka k'ulla na munafunci. Koda suna cikin habaice-habaicen su ne Fad'ime ta fito tsakar gidan nan za su ɓige da shewa suna watsamata bak'ak'en magana a fak'aice. Ko kallon inda suke Fad'ime ba ta yi balle su saka ran za ta tankamusu.
Ranar wata laraba wanda ya yi daidai da cikar Inna kwanaki goma sha shida a birni, Abule da Nene suna zaune a gaban d'akin Abulen suna k'us-k'us tare da Shafa makwafciyarsu. Shafa ke yi musu tallar magungunan gyara na mata kala-kala. Ta d'aga wani k'ullin gari tana fad'in.
"Kun ga wannan? Na rantse da daren farkona da jikan Lamid'o yana da masifar kyau. Ke wannan da ku ke gani sunansa 'Saki Matar Uba'."
Nene da ke soshe-soshenta ta dubi Abule suka yi wata iriyar shewa gami da cafkewa.
"Inda ranka ka sha kallo! Yo Allah na tuba idan kura na magani ta yiwa kanta mana!" Fad'in Abule.
"Atoh, taya ni gani! Wai Matar kwarto da tallar maganin mata." Nene ta cafke.
Jin haka ya sanya Shafa kallonsu a fusace kafin ta d'an kalli d'akin Fad'ime, ga dukkan alamu batasan ma me suke yi ba. Ta maido dubanta gare su cike da borin kunya ta ce.
"Oho dai, gwara ni akan ku, haka za ku k'arata a borori."
Ta hau tattara komatsanta a sadda suka yo mata ca! kowannensu da bak'ar maganar da yake yarfamata. A daidai nan kuma Faɗi ta fito daga ɗaki da gudu zuwa bakin makwararar tsakar gida ta hau sheƙa amai kamar ba gobe.
Nene ta miƙe ido waje tana tafa hannu, yayin da Abule ta dafe kirji tana duban Faɗi dake duƙe.
"Duka-Duka yau kwana nawane da Auren ni Nene? Taya ni lissafi Abule.
Abule ta hau kasafta yatsun hannunta, sai kuma ta zare ido waje.
"Duka-duka kwana goma sha bakwai kenan, kar dai da ruɓaɓɓan kwai aka shigo?"
"Oh ni Nene, wannan wace irin haɗama ce haka, ranar farko da rabon ciki kamar marainiyar Karya? Ke kuma maƙaryaciya kika cemin ba ai komai ba ranar jikin tagarsu kika kwana?"
Abule ta ɓalla mata harara, "tuna dai, ke kika cemin ranar da aka kawo ta jini take, koma dai menene ni ban yarda da wannan Salon ba, ban taɓajin cikin dake bayyana kansa daidai da lissafin zuwan Amarya ba. Sai dai idan da shi aka shi..." Nene ta yi Wuf! Ta rufemata baki jin sallama kamar ta Inna.
"Barta ta ƙarasa mana manyan Akuyoyi, ai na dade tsaye ina sauraronku, wanda ya gani dai shi

ya ji kunya wai kallon fitsarin makaho. Idan ba ku da kuke cikin ƙauye, haihuwar ƙauye, renon ƙauye, auren ƙauye, ina na taɓa ganin ana laɓewa sabuwar Amarya? Kunyi asara wallahi Nene, matsa ni na duba 'yar mutane, shashashai masu wankin kai da ruwan daddawa, idan ma da cikin ta shigo sai me? Na ce sai ƙaƙa? Irin kune a jahannamar ma can ƙasan wailun kuke. Sannu 'yarnan, sannu."
Inna ta k'arashe tana mai k'arasawa ga Fad'ime wacce aman ya d'an lafawa.
Gefe guda ta ajiye akwatin kayanta, ta yaye gyalenta ta dora saman akwatin kafin ta tattare zaninta dinkin rafa siket. Ruwa ta zubo a buta gami da mik'omata.
"Tayani duba Abule, toh wallahi ba za ta saɓu ba bari Matin ya zo, ni ban yarda wannan cikin nasa bane, ga dukkan alamu dai mutum da abinsa ya zo, ai daman ni nasan za'a rina, angama yawon ta zubar an k'untso.."
"Ki ka k'ara magana a wajennan sai na nunamaki ni ce nan na isa da Mijinki don kuwa yana zuwa zan sanya ya sallamaki ga tsohonki."
Nene ta yi d'if ta ja hannun Abule wacce ranta ke ƙuna suka fad'a d'aka. Shafa kuma da ke gefe kunne waje, tayi saɗaɗa ta fice daga gidan.
"Mun shiga uku Abule, yanzu idan ta tabbata matarnan juna biyu gareta ya za mu yi?"
Fad'in Nene kenan yayinda gumi ke tsirfomata. Abule wacce ta rasa bakin magana tsabar bakin ciki da tashin hankali, sai a lokacin ta iya bud'e bakinta ta ce.
"Hum, ni na rasa ma abin cewa wallahi."
Sallamar Mati ce a gidan ta katse su, suka  yi shiru suna sauraron yanda Inna ke gayamasa rashin lafiyar Fad'ime da kuma cewar Fad'imen na tunda ta zo ba ta ga Al'adarta ba.

Page

*GIDAN MATI*
BY BINGEL FULANI & RUFAIDA OMAR
Kamar wasa cikin Fad'ime ya tabbata, Inna har Asibitin K'auyen ta mik'a ta tare da Abule da Nene wadanda suka tik'e akan sai sun bisu sun ji da kunnuwansu. Itama Innar ba ta yi gigin hanasu ba don ta fi so su ji abinda zai hana su bacci.
Ranar kam sun riga su yin gaba, zagi da tsinuwa ba irin wanda Fad'ime da Inna basu sha ba. Tun daga wannan lokacin kuma sai sabon tashin hankali da makirci ya k'ara ɓallewa a gidan. Akwai ranar da Nene ta shigo da Kuliya cikin gidan, sanin cewa Faɗime ba ta so. Hakanan ta lallaɓa ta  d'ora mata ita bisa gadonta tana cikin barci. Allah ne ya tsare da kwallayenta na jere basu zubo bisanta ba, saboda yadda ta dinga razana tana bige-bige a ɗakin. Ƙarshe dai Inna ta cece ta da fitsari ya fiddo ta, ta juyo motsi ɓarin Faɗimen. Shi kuwa Mati yana can ya saki gañɗa ɗakin Abule. Sai washegari ne Inna ta sanar masa, karshe dai ta yi maganin abin da cewa duk wacce ta k'ara kawo wani Abu gidan ko da Ɓera  ne, ko ta jefi Faɗime ko Mati da bak'ar magana to a bakin aurenta. Da wannan aka samu bakinsu ya rufu suka koma rara  gefe, ƙarshe dai Nene ta tattara ta tafi wani ƙauye bikin kanwar kishiyar matar babanta.
Inna zaune gefen Fad'ime tana lalla6ata ta samu ta ci kwad'on Zogalen da ta had'amata, ita kuwa Abule tana tankad'e Garin Tuwo tana wak'e-wak'en habaici. Fitowar Nene daga bayan gida ya sanya suka bita da kallo. Tayi daurin k'irji da tsohon zanin da ta ci 'yanmatancinta da shi duk a huje, k'asan duk ya rarake har idan ka zura hannu a 6uli guda zai ta6o mazaunanta.

Fatarnan kallo daya za ka yi mishi kasan akwai nakiyayyar d'aud'a da bai kammala fita ba, jikinta kuwa babu alamar ya wanku. Sai kyalli takeyi da nason datti da hamami dake tashi.
"Ke jik'ar Maduga, wai wankan da ruwan Taɓo ki ka yi shi ne?" Cewar Inna.
Juyowa ta yi ta mata murmushi, sai kuma ta yi gaba tana murzo wata naɗaɗɗiyar dauɗa a wuyanta.
"Ah'ah Nene magana fa nake miki." Fasa ɗaga labulen kabar ta ta yi ta juyo tana kallon Innar, sai kuma ta haɗe mata hannuwa biyu tana roko alamun ta kyale ta.
"Uhm! Sabon salo, wai gemu a kafaɗa, halan da kika je bikin rashin magana kika koyo? To ai gaba ta kai mu, tuntub'en me carbi" Inna ta faɗa tana riƙe hab'a.
Ganin haka ya sa Abule ture tankaɗen gefe, ta mike zuwa dakin Nene.
Da shigarta ta same ta tsaye tana jan Jagira a girarta me kama da ta Tunku. Ai sai ta yi turus! Da mamaki tana ƙare mata kallo daga ƙasa zuwa sama. Ta sha Atamfa koriya fatau, da dinkin rigarta irin na Lema, wani abin mamakin har kallabin irin na atamfar ne, ba wai wari da wari ba. Kwalliya dai irin wacce ko da tana Amarya ba ta taɓa yinta ba. Sai ƙamshin man kadanya ke tashi da ta mulkawa jikinta.
"Wannan kallon fa? Ban fa san irin kakannin ki ba?" Ta faɗa tana kaɗawa Abule hannu ganin yarda ta ƙame.
"A'a mamaki kawai nake, tunanina ko dai ƙanwar Nene aka  musaya mana.
"Uhm! Kibar mamaki, kawai nasihar da Innata tamin kan zaman duniya da ƙiyama nake ta tunanowa yau."
"Anya kuwa Nene? Ke din ce kike tuna wanda ya mutu? Abokin kuka ai ba a ɓoyemasa mutuwa. Ki faɗamin abinda ya faru dake kika saki makaman haka? Ko duk tsoron kar Innar Mati ta kora ki gida ne?"
Ai sai ta gundumo ashar tana me ture ɗaurin kallabin da ta dade tana murd'ashi dan ya yi kyau gefe. "Ni wallahi har kin ɓatamin rai, tsohuwar banzar can zan ji tsoro? To Talle Bodara ce ta ba ni maganin Ɓari, sharuɗɗan cikar maganin shi ne ko daka Ni Uwar Miji za ta yi kar na sake na tanka ta. Kin ganshi a bakin Masai ake barbaɗashi."
Ta karashe gami da bankad'a k'asan katifarta, wani k'ulli ta fiddo a bak'ar leda ta nunamata. Abule ta washe baki don tsabar farinciki. Ganin babu damar ihu ya sanya ta kaiwa Nene runguma sai dai tun kan ta k'ara sa had'a jikinta da na ta ta yi baya da sauri tsabar tashin da Nene ke yi kamar mai warin k'ashi.
"Dagaske ki ke yi?"
Nene ta ta6e bakinta.
"Ni idan na fad'i abu na fi son ki yarda, zan miki k'arya ne? Nan da ki ke ganina ba ta wasa bace ba. Bari ki gani, wuyarta dai Fad'ime ta tsugunna saman Masai, ko kwad'o ne a cikinta sai ya fad'o.
Jin haka suka saki shewa gami da cafkewa, sai kuma da sauri suka rufe baki.
"Um kinga bari na je kafin wannan Tsohowar karuwar birnin ta ankara."
Dariya Nene ta yi.
"Ai mukam Allah Ya had'amu da suruka."
Suka dara sannan Abule ta fice.
***
Shiru-shiru ciki zai zube anjima, gobe, bai zube ba. Ko ciwon kai Fad'ime ba ta yi ba ballantana

a kai ga ciki.
Ganin haka Abule ta yanke gwada ta ta sa'ar ko za'a dace. Nene ta ba ta goyon baya d'ari bisa d'ari, da wannan ta shirya tafiyar kwana daya da sunan ziyartar jikar abokiyar kakarta.
Dawowarta akayi sa'a babu kowa sai Nene a gidan da ke faman zazzaga bala'i ta katanga tare da Delu wai Akuyar Delun ta shigo ta cinyemata shanyar da ta yi ta k'anzo.
Ganin Abule ba k'aramin dadi ta ji ba, itace har da rungumarta tana tsalle, da ace akwai mutane a gidan da sun sha mamaki.
Bayan sun k'ule a d'akin Abule ne ta hau bata labarin abinda ta samo.
"Ba k'aramar wuya na sha ba in fad'amaki. Ban ta6a rawar 'yan bori ba amma shege la'antaccen bokannan sai da ya sanyani yi. Amma tunda kwalliya za ta biya kud'in sabulu da sauk'i. Bari ki gani."
Ta ɓalle ɓarin zaninta ta fiddo k'ullin magani har biyu ta nunawa Nene.
"Ya ce na kwa6a lalle da garin na d'aurawa Inna a k'afa don rufe bakinta. Shi kuma wannan."
Ta nuna d'ayan,
"A had'a Lemon Zobarodo a sanyawa Fad'ime a ciki ta shanye."
Shiru ya biyo baya kafin Nene ta jinjina kai.
"Tabd'ijam! Aiki ja! Yanzu banda abinki ina mu ina iya haka? Ni kinga banda kwaɗa zobo da kuli ba abinda na sani kansa, sai yau da na ji ana lemonsa, kema kuma na san duk sammak'al. Inna kuwa ba ta yanda za ta amince waninmu ya d'auramata lalle. Ina mafita?"

Page 9

"Ke dadina dake jahilci kwarankwatsa dubu, haba ai ko karamin yaro ya san ruwa za a shekama Zubo a zuba Sugar shi ke nan ya zama lemo, batun lalle kuma kin manta Inna da shegen san fadanci kamar matar Bawan Sarki? Ai kawai kururuta mata kai zakiyi har ta sake ta baki kafar ki kunsa. " Nene ta yi shiru kamar mai nazari, sai kuma ta gintse fuska ganin Fad'ime ta fito zuwa makewayi. "Shegiya kai da wata fuskarta kamar taunanniyar gyada, Allah Abule yadda naki jinin Matar nan bank'i a cemin karta fito raye daga makewayin nan, ba ni zoban ki gani duka gidan zan had'a idan ya so a na tan sai na juye maganin" Ta fad'a tana wartar ledar zobon da Abule ta riga ta siyo. "A'A hankali dai Nene d'an kad'an ya ce a zuba saboda karfinsa." Ta balla mata harara "Wallahi duka zan juye idan za a sha giya asha ta dubu Abule!" Ta fad'a tana mai ficewa daga d'akin. Kai tsaye madafi tayi ta dauko kwanon sha ta juye zobon, ta tuttulo ruwa daga tulu ta sheka bisansa ta zuba Sukari wadatacce ta juya. Nan da nan ta kasafta na kowa, na Inna ta fara dauka dauka za ta kai mata, da shigarta kuwa ta tarar ta tana gyangyadi dan haka ta aje ta juya za ta fita. " Na shige su ni Uwar Biyu, Nene me nake gani haka?" ta juyo da sauri tana kallonta kafin kuma ta saki murmushi. "Zobo ne muka samu tsaraba daga Abule, shi ne na hadamana lemo da shi na san ai kin sanshi a birni." Inna ta balla mata harara tana turo kallabi goshi." To ke ina kika taba ganin anyi zobo ba a tace tikar ba? Wannan zobo za mu sha ko roman zobo? Idan ba ku iya abu ba ku dinga tambayata mana, ni nan da kuke gani na bayan zobo durinkis (DRINKS)har mangwar durinkis (MANGO DRINKS) Na iya, dan haka ban san jahilci d'auki ki ta ce shi sai ki kawon. Sum-sum Nene ta fice jin Inna ta koma yaren 'yan sama jannati. Sake gyarawa ta yi, tukun ta dauki na Fadime ta kai mata daki, komawarta daki ke da wuya Mati ya sawo kai Gidan. Kai tsaye dakin Fadi ya yi yana doka

sallama, fasa kai dan karamin kwanon shan baki ta yi ta aje tana amsa masa da murmushi kafin kuma ta mike tana kokarin zare masa zungureriyar hular da ke kansa. Ya shaki kamshinta da yake so na Karkar dan haka ya washe baki "ALLAH Amarya son ki nake kamar na mutu" Ta yi murmushi tana rangwada kwalelen kanta "A'A Maigidana mai ya kawo mutuwa kuma, muna tare ai." "Hmm! Ba za ki gane ba ne, idan kina kusa da ni ji nake kamar numfashi... KYYYATTT...FYYTTATAT... Ya dakata yana mai kakalo kaki, kafin kuma ya dunkulo majinar yana mai furzo ta waje da ba ta dire ko'ina ba sai cikin kwananshan Fadime dake cike da zobo. Ita da shi suka zubawa kwanon ido kafin kuma ta kwabe fuska. "Haba Maigida na sha ce maka ka dainamin tofe-tofe a bangon daki ko kasa, wannan ko a kan titi ne ba abin so ba ne. Yanzu kalli yadda ka haramtamin abinda tunda na gani yawuna ke tsinkewa. " Ki hakuri na mantane, yanzu bari na karbo miki kasona sai ki sha." ya fada yana mai daukan kwanon ya fice. Bisa randa ya tadda wani kwanon rufe da Fai-Fai Dan haka ya aje wancan ya dau wannan ya tafi. Nene da ta shiga makewayi rage ciki tana fitowa tayo inda ta ajje zobanta, ganinsa bude ya sata doka ashar "Ko wane shegen ya budemin oho, to idanma diba akai an sha wuta bal-bal tunda nawa ne. Ta fada tana hararar dakin Inna, kafin kuma ta daga kwanon ta kwankwade tas! Har kakin Mati. Minti biyar da sha cikinta ya yi wani irin juyi, jin kamar ruwa da wani wari na binta ya sata lekawa abin da ta gani na binta ratata ya sata doka ihu tana dafe mazaunanta "Wayyo ni Mati! Yoyon Kashi ya kamani.

Page 10

Ihun Nene ya janyo hankalin mutan gidan, gaba daya suka fito har da Abule wacce ta gwaggwa6e a d'aka tana kwa6a lallen. Kan kace me tuni Delu ta gyara zamanta jikin garu tana lek'e, itama Shafa ba'a barta a baya ba wajen ganewa idonta. Mati a rude ya nufeta.
"Nene, lafi..."
Kii! Ya ja burki sakamakon wari da k'arar sakin tusa da ya bugi kunnuwa da hancinsa. Inna ta sanya salati.
"Me zan gani haka Nene? Wane irin shashanci ne haka ki wuce Makewayi mana" Nene dake ta kokarin danne mazaunanta da hannu ta daddage ta ja numfashi sama tana mai hade jikinta dan ta tsayar da gudawar, ganin kamar an kara kunnu ta ya sa ta sakin wani wawan ihun "Wallahi ba ta tsayawa, na shiga uku ruwan jikina zai k'are. Kai Mati! Kai mati zan mutu, za ta zuƙen jini" Ai sai ta zabura ta danna a guje zuwa karshen gidan abu na yoyo. Mati ya yi sauri ya bita ganin ta zube gun, "Nene, nene, jin shiru ya sa shi toshe hanci yana jijjagata, sai kuma ya dago a tsorace yana duban Inna.
"Kamar fa ba ta numfashi Inna" "kai kauce nan, wane irin ba ta numfashi matsa ni ka ga na ba ta fastu aidi (First Aid)shashasha ko dabarun lafiya baka iya ba dake kanka ya cika da gashin jakai." "Um Inna yanzu dai bata ba'a ake ba ki duba ta kiga ni Aradun Allah Inna ba ta motsi" Inna ta dan na masa harara, sai kuma ta hau karewa Nene dake yashe kallo, ganin har yanzu Abun na tuttulowa daga jikinta ya sa ta kallo Mati "Tunda dai kai ne Mijinta matso kusa daidai bakinta ka lalubo harshenta ka gantsara mata cizo, shi ne zai sa ta farfadowa yanzu" Mati ya kalli Inna da ta kauda kai gefe tana jijjiga kafa kamar ba ita ta fadi wannan zance ba, ya waiga ga Abule dake matsar kwalla, ya dora idonsa kan su Delu dake bisa katanga, ai sai ya hau girgiza kai yana mai sharce gumi "Bazan iya ba! Kwarankwatsa dubu Inna wannan zalunci ne,

ya zan ciji marar lafiya. Kuma sannan wannan ai Yahudanci ne." ai sai inna ta zabga salati tana mai fashewa da kuka Mati ya ce mata Azzaluma, kafin kuma ta share hawayen tana mai watsa ma masa dakuwa "To ka tsaya jahilci Nenen ta mutu, numfashin mutum na daukewa da minti goma idan bai samu taimakon gaggawa ba yake mutuwa"
Jin haka ya sa Mati yin wurin Nene da sauri yana lalumar bakinta. Da dai ya zakulo harshen ai sai ya gatsashi da karfi. Baya ya yi yana ganin Nene ta yi wani irin cilla kafa. Tana fadi a hankali " Na mutu Mati" cikin magagi. Abule ta ƙara sautin kukanta "Inna dan Allah mu kai ta gun kula da lafiyan da kika kai Faɗime kwanaki" Mati ya kalle ta, sai kuma ya yi waje da sauri. Ba daɗewa sai ga shi da mai Baro. Abule ta taya shi kama Nene aka dora ta bisansa. Suka ɗunguma Asibitin ƙauye.
Bayan dube-duben da likitan ya yi sakamako ya fita. Nene dai banda Maleria ba abinda ke damunta. Likita duk tambayoyin da ya yi sun tabbata ba abinda ta ci na ɓata ciki tunda dai abincinsu guda ne. Dan haka ya daura ma karin ruwa ya rubutawa Mati O.R.S da Napkin na manya aje a siyo mata. Ta kuma dinga daura napkin din duk bayan sa'a biyu. Karshe ya sallemusu da cewar su je Binni a duba ta da kyau shi kam iya na sa ke nan. Da komawarsu gida Abule ta yi wuf! Ta fada ɗakin Nene tana sakayo kaba. Kallonta take cike da tausayi ganin harta tsotse rana guda.
"Ni Nene anya ba maganin fadi kika sha ba? Na ganta sumul fa" Nene dake ji da yoyon kashinta ta mike a hankali jiki na rawa" Shi ne wlh a randa na tadda shi a bude na sha, na shiga musanyamin ta yi bakar muguwa wayyo ni. Mene makarin ki taimake ni Abule" Abule ta dafe kirji ido warwaje "Lalle dara ta ci gida Nene! Makarin da wuya Nene, ba za mu iya ba, sai kuma rushe da kuka."
Nene ta yi ruf da ciki tana numfarfashi.
"Ki fad'amin Abule, ko menene shi zan iya."
Jin haka Abule ta fyace majina ta soma magana.

Page 11

Abule ta yi k'asa-k'asa da murya.
"Makarin shine a jik'a wandon kwarto a shanye."
Nene ta zabura tayi zaman 'yan bori wanda ya yi daidai da sullu6owar tusa ta mai k'ara. Abule ta toshe hancinta, a hankali Nene ta numfasa har da lumshe idanu don ba k'aramin sassauci ta samu a cikinta ba.
"Na shiga uku, yanzu ina zan ga kwar... Af! Fad'uwa ta zo daidai da zama ai Abule, yo bana manta ashe muna da su a kurkusa ba? Ga Basharin Shafa?"
Abule wacce itama shaf ta mance da batun Jik'an Lamid'on ta sauke ajiyar zuciya tana mai jin zuciyarta wasai, babban abinda ya sanyamata damuwa da lamarin ba komai bane sai na tsoron kada ya kasance Nene bata warke ba ta tonamata asiri mutan gari su zageta. Ta daki cinyarta tana mai washe rinannun hak'oranta.
"Kai Allah mungode maka, ai ni dinma kaf tunanina bai je nan ba. Ko jiya da daddare ya haurawa Kulu Gurguwa."
Suka saki shewa don Nene har ta hango warakarta a sauk'ak'e.
"Kai Allah Ya k'arowa Bashari ilimin kwartanci, wannan ai gaba ta kaini. Ashe kwarto da

ranarsa. (Kun ji jahilci!)"
Dariya suka k'ara kwashewa da ita.
A yammacin ranar Shafa na durkushe a gaban murhu tana kokarin iza wuta ta tsinkayi sallamar Nene da Abule. Da mamaki ta dubesu kafin ta mike. Abule ta ci burki anan tana k'arewa gidan Shafar kallo domin rabonsu da shiga gidan har sun mance. Daga can gefen garu ta hangi jerin manyan duwatsu wanda ta taimakonsa ne Shafa ke k'arewa cikin gidansu kallo. Ta6e baki ta yi gami da bin sahun Nene da har ta shige rumfar Shafar ba tare da ko neman izni ba.
Shafa za ta yi magana Abule ta hanata ta hanyar rik'o hannunta tanamata alamar ta yi shiru gami da yi mata nuni da gidansu, nan take ta fahimci ba su kaunar Fad'ime da Inna su san da zuwansu. Ta gyara zaman d'aure kirjinta suka shige ciki.
Nene ta washe baki.
"Shafa Shafa, Shafar Bashari, uwargida ran gida! Kin tare gaba kin tare baya, turmin tsakar gida sha lugude!"
"Wannan haka yake." Fad'in Abule tana gyada kai kamar k'adangaruwa.
Shafa ta yamutsa fuska tana kallonsu d'ai-d'ai.
"Halan dai Nene acan asibitin har allurar mahaukata suka manta suka yi maki?"
Nene ta hau daure fuska za ta kwa6omata mai zafi ganin haka yasa Abule saurin tarewa.
"Kai Shafa, dad'ina da ke zolaya. Nene ai taki ce, banda abinki ai makwafci ance ya fi dan uwa, a baya ma rashin fahimta ne."
Dariya Shafa tayi gami da tafa hannuwa. Nene da Abule suka dubi juna, dakyar dai suka shawo kanta ta yarda zata sauraresu.
Nene ce ta soma magana bayan ta gyara zaman nafkin dinta.
"Ki taimakeni Shafa ki bani aron wandon Bashari."
Shafa ta fiddo idanu gami da dafe k'irji.
"Yau naga ta kaina! Nene me zakiyi da wandon Basharina? Anya Nene ba ki samu matsalar kwakwalwa ba? Au to na fahimta, wato dai duk matattarar kwararar gudawar da aka sanyamaki bai isheki ba sai kin had'a da wandon Basharina? To mine amfanin na Mati?"
Nene ta share zufa tana girgiza kai. Abule ta cafke zancan.
"Kinga Shafa duk ba haka bane, wannan maganar da za mu yi sirri ce, don Allah ki rufamana asiri."
Shafa ta dan zubamasu idanu na 'yan dak'ik'u kafin ta gyada kai don ba za ta bari gulmarnan ta wuce ta ba.
"Ina jin ku."
Abule ta zayyanemata duk abinda ya faru da kuma makarin asirin.
Shafa ta saki shewa har da tafa hannuwa.
"Yau abin namu ne! Oh ni matar na Lamid'o!"
Saida ta basu wuya Nene harda matsar kwalla sannan ta amince da sharad'in Nenen za ta kyautarmata da tunkiyarta da take kiwo. Ba musu Nene ta aminta daganan ta mik'e ta fita zuwa d'akin kwanansu ta hau lalube.
Jimawa kad'an sai ga ta rik'e da wani tsohon wandon Bashari da ya gada gun Lamid'o ta mik'amata.
"Gashinan, kuma kada ya kai gobe a wajenki, ko ta katanga ki jehomin."
Nene ta hau godiya kafin kuma cikin lallami ta ce.

"Ki taimakamin Shafa, ki bani sabon d'inki mana."
"Cab! Ai idan kinga Bashari ya yi sabon dinki to mutuwa akayi a danginsa don haka ban bayarwa, idan ba kwa so ku k'ara gaba."
Ta k'ara he tana girgiza k'afa gami da jefamusu tafin hannunta.
"A'a me ya yi zafi? Mu je Abule hakan ma ya wadatar" " To karki manta dai ki jefon ta katanga."
Da komawarsu kuwa Abule ta tarkata lallen ta watsar Masai, shi zaman duniya dama rabo ne, idan ba ka da shi kuwa za ka zo ne a banza ka koma a wofi. Tuna hakan ya sa ta nutsuwa ta ma fita daga batun Fadi. To haka ma ga Nene sai wayar gari akai aka ganta sumul tamkar mai bugun Iska. Itama ta mai da rayuwarta shiru ta hanyar aro nutsuwar dole. Daga bisa ni ta kulla Amintaka da Shafa ba ma ta zaman gidan balle ta zubda hali. Bayan watanni, ranar wata laraba wanda ya yi daidai da kwanan Inna guda a birni ta je hado kayan haihuwar fadi. Faɗimen ta tashi da nakuda. Gidan daga Abule sai Nene dake shirin fita.
Ta gyara zaman yafenta tana mai sauke kabar shiga d'akinta. Ta juyo gami da duban Abule, za ta yi magana kenan suka ji nishi da salatin Fad'ime. Cikin hanzari suka dubi juna.
"kinji abinda na ji?" Abule ta ya tsina fuska" na ji mana kila abinne ya zo." "To ya za ai ko mu dubu yar magaji... " Abule ta yi saurin rufe mata baki. "Ke gafara, kinmanta yanda ta musanya miki magani? To yaune ranar ramuwa dan haka maza kwaɓe gyalen nan ki dauka surfe mu yi yanzu dan karma makota su jiyo bayan awa guda ma lekata." Da sauri Nene ta aje gyalen ta juye hatsinta a turmi suka hau dukansa ba ka jin karan komi sai tunkwal-tunkwal.
Fadime cikin azaba haka ta rarrafo bakin kofarta tana kiransu amman suka yi biriss da ita. Har sai da suka bar jin muryarta tukun suka zubda taɓaren suna ma su nufarta. Ganin ruwa gefenta ya sa Nene zare ido "Ke abu ai fayar ta fashe."
Abule ta karasa itama tana lek'e-lek'e, a karshe suka kinkimi Fad'ime suka maidata ciki. Haka suka kar6i haihuwar santalelan d'anta suka yanke cibi. Nene dake rike da jaririn wanda bai bar komai na Mati ba, katon kan Fad'ime ya yo. Ta yiwa Abule ido kafin ta fice zuwa d'akinta rike da jaririn wanda ta cusawa yatsanta a bakinsa gudun kada sautin kukansa ya ankarar da gulmammun makwaftansu.
Abule ta dubi Fad'ime wacce ba k'aramin k'aruwa ta samu ba wajen haihuwa sai murk'ususu ta ke da alamar dai akwai abinda ke damunta. A hankali ta sulale ta bi bayan Nene. Idanu ta ware a tsorace ganin Nene na kokarin sanya jaririn cikin kwali.
"Nene! Bakya tsoron asirinmu ya tonu?"
Nene ta harareta.
"Kinsan iyakar tsawon lokacin da na dauka ina ajiyar kwalinnan? Ai bazan bari damarnan ta kufcemin ba, yau dan kwal ubannan sai kwanan daji."
Kafin Abule ta ce wani abu suka tsinkayi sallamar Mati.
A razane suka dubi juna har Nene batasan sadda ta cire yatsanta daga bakin jinjirin ba ai kuwa ya canyara kuka.
"Lafiya Fad'i? Kin haihu ne?"
Mati dake jefowa Fad'insa tambayoyi ya tsaya gami da saurin bin inda ya jiyo kukan jaririn. Duk kokarinsu na kada ya fahimci shirunsu saida ya gane. Nan ya hau salallami, wani wawan tsalle da ya doka sai gashinan gaban Nene, ya kwasheta da mari kafin ya fiddo jaririn daga kwali.
"Ka gantanan, yasin ba hannuna ciki! Yanzu na shigo daga makwafta ina.." Fad'in Abule

yayinda Mati ya katseta da sauri.
"Dalla can rufemin baki kema bakar munafuka! Wato kun yi shirin kashemin mata da d'a ko?"
Sautin karar Fad'ime ya kid'imashi, a guje ya fice zuwa d'akinta.
Kan kace me Shafa da Delu sun shigo domin tun kukan jaririn na farko sun tsinkaya saidai ba su k'ara ji ba sai yanzun da Mati ke balbalin fad'a. Lek'owarsu suka san abinda ke faruwa suka bazamo cikin gidan.
Su ya bari a wajen Fad'ime yayinda ya fice nemo abin hawa don mik'a Fad'ime asibiti.
Delu na gyara jaririn tana zubamusu habaici Shafa na tayata. Su kam kowacce na d'akinta sun k'unshe gaba daya a tsorace suke da abinda zai biyo baya.
"Shegen, ashe d'agamin k'afa kawai ya ke." Fad'in Nene a k'asa-k'asa tana shafa kuncinta.
Mati na dawowa aka wuce kai Fad'ime ga likita bayan ya kora Nene da Abule gidajensu da shika (saki) d'ai-d'ai.

Page 12

BAYAN WATA GOMA
Rayuwa mika a gidansu Mati, abubuwa da yawa sun faru ciki harda dawowarsu Nene bayan sunyi Bikon Mati sau kusan goma. Wanda Nene sai da ta koma yini a gona gun Mati tsaban son ta koma dakinta. A rana sai tai wanka sau hudu ko biyar. Goge hakora kuwa masu sai da gawayin ƙauyen sai da suka shaidata, haka ma masu Gishiri. Saboda tsabar tsafta sai da ta koma yawo da tsumma tana goge kafarta idan tai kura. Wannan fa duk shawarar ƙawarta Shafa ce. To haka ma ga Abule itama sosai ta nutsu dan har dan abin kwalama take kaima Mati gona. Musamman ma Kundun Kaza da ta san yana so. Karshe dai ya mai dasu. A daren Inna ta tarasu da ta ta nasihar ta nunamusu laifinta ne tare da neman gafararsu.
"Haba Inna, ta ina kika zama mai laifi? Mu keda laifi mu yakamata mu nemi gafara."
Fad'in Nene kenan tana mai k'arashewa da sheshshek'a.
Fuskar Inna cike da damuwa ta girgiza kai bayan ta k'aremusu kallo gaba daya har Matin tana mai shafa kan jikanta Atiku dake saman cinyarta, ya sha billensa a goshi an rambad'amasa kwalli yayinda fuskar ke ta kyallin mai. Ta cigaba da magana.
"Um um Nene, bari fad'in haka, maganar nan haka take. Abule da bakinta ta sanarmin musabbin wannan rashin jituwar a sadda take zuwa yawon biko, nayi kuskuren ware wani kaso na dukiyata da zummar bawa jikan Matina na farko, kai kuma Mati bai kyautu ace kai da kake Maigida ba kana nuna halin k'aranta, Abule ta sanarmin da irin yanda ka sanyata k'aryar ciki wanda tun daga ranar zaman lafiya ya k'ara k'aranci a gidanka. To yanzu wannan sai ya zama izna gareka, matuk'ar kana son had'in kan iyalanka kada ka k'ara wannan gangancin. Nima a karshe ina neman gafarar..."
Da sauri duk suka tari numfashinta kowa na kara neman gafararta, Nene da ke tashin k'amshin turaren matan arewa ta rungumo kafadar Abule dayan kuma ta rungumo Fad'ime wacce farinciki ya cika don har zuciyarta bata son fad'ace-fad'ace, washe bakinta ta yi wanda ya sha durji da gawayi ta ce.
"Yanzu mun zama tsintsiya mad'aurinmu d'aya. Daga gareni Nenen Mati babu abinda zai k'ara fitowa daga wurina."
Farinciki ya cikasu babu ma ya Mati wanda har aiken kiss ya yi musu ta iska bayan ya fakaici

idon Inna, suka tuntsire da dariya kuwa.
Cikin iko na Ubangiji kuwa tun daga ranar babu hayaniyar da ta k'ara tada hankula a GIDAN MATI, Nene a matsayinta na babba ta ja girmanta da sauran mutuncinta da ya rage, hakanan Fad'ime tana binsu sau da k'afa, saida ya zamana rainon Tanimu ya koma ga Nene, kai kace itace ta haifeshi. Fad'ime me kawaici kuwa ta d'auke kanta daga Atiku, muddin ba nono zai sha ba to fa babu abinda k had'asu sai kwanciyar bacci. Bangaren Mati shima kuma daidai gwargwado yana kokarin yin adalci tsakankaninsu. Wannan ya kwantarwa Inna hankali.
SAUYIN RAYUWA
Gida ne wanda ya sha filasta madaidaici, tsakar gidan an shafeshi da sumunti. Dakuna ne jeras har hud'u sai falo babba guda daya wanda daidai talakan k'auye ya tsaru.
Nene ce ta fito daga d'akin dake jikin na maigidannasu tare da Atiku da kanwarsa Sa'a, ta cakare cikin atamfa mai kalar ruwan masara, tana kokarin rufe k'ofar d'akinnata bayan ta saki hannun Atiku ta ce.
"Wai mutanennan kuna so dai dare ya yi mana ba mu tafi gidan bikinnan ba ko? Abule! Kanwata!!"
Kusan a tare suka amsa gami da fitowa daga d'akunansu sanye cikin atamfa irinnata. Abule rik'e da d'iyarta da Allah Ya bata wacce ko wata shida bata cika ba a duniya yayinda Fad'ime ke goyon yaronta na uku Sallau don Nene kam Allah bai bata ba.
Nene ta washe baki.
"Inye, cakarewa. To ai ni har kun fini kyau."
Suka dara.
"Wane mu?"
Fad'in Abule da ke saita zaninta. Suka rufe ko'ina suka jera gidan Delu wacce ke aurar da yanmatanta uku.
Kowa a gidan bikin ya yaba da shigarsu,  Shafa ita kanta ta yi kyau tamkar ba ita ba, cikin hukuncin Allah mijinta Bashari ya shiryu ya daina kwartanci, hakanan Delu itama mijinta ya daina dukanta tun watarana da diyarsu Bushira (wacce duk cikin yaran ya fi kaunarta saboda nutsuwarta) ta gwada d'aga hannu da zummar ramawa uwarsu, wannan abu ya dagamasa hankali ainun karshe dai ya saduda bayan limamin garin ya shiga lamarin ya mishi nasiha.

TAMMAT BI HAMDULLAH